"AREWA"



Daga Ina, Zuwa Ina?

Bashir Othman Tofa

July, 2011

AREWA:

Daga Ina?

Zuwa Ina?

A ra'ayin

Bashir Othman Tofa

Na ba da iznin a buga shi yadda yake, ba canjin ko da kalma ɗaya,

A rarraba kyauta ga duk waɗanda yakamata su karanta shi.


Idan ana son irin wannan darajar ɗab'in, sai a kaiwa:

"CLEAR IMPRESSIONS", SHARADA, KANO STATE.

KADA A SAYAR

ABINDA KE CIKI

		Shafi
1.	Godiya	5
2.	S.1: Gabatarwa	6
3.	Lalacewar Al'amura	21
4.	S.2: Zubewar Mutunci	28
5.	Shawarwari	35
6.	S.3: Arewa a Nigeria	42
7.	Karshen Magana	63
8.	TUNATARWA	65



TASAWIRAR AREWA (a NIGERIA)

1. Dukkannin shacin da yake sama da jan layin, Arewa ce.

2. Idan aka raba fadin Nigeria gida 4, Arewa ita ce kusan kaso 3.

3. Arewa ba ta da gaba da teku, amma zata iya shigo ko aikawa da dukkanin kayanta daga kasashen makwabtaka; ko ta hada hanyoyi daga Katsina zuwa tashar ruwa a Morocco. Haka kuma, daga Borno zuwa tashar Port Sudan.

4. Ba abinda Arewa take bukata sai zaman lafiya da hadin-kai

Godiya

Da sunan Allah Mafifici, Mafi ɗaukaka. Muna roƙonSa Ya sa mu gane abubuwanda suka fi mana alhairi, mu yi aiki da su. Mu gane abubuwan da suke sharri ne garemu, mu kauce masu. Ina roƙon Allah Ya daidaita tunanina yadda zan yi jawabin da zai amfanar, ba tareda na ɓatawa ko muzgunawa wani ko wasu ba. Haƙiƙa, ɓatawa da muzgunawa ba sa cikin niyyata. In haka ta faru, toh, Ina neman gafara saboda Allah.

Ina kuma isarda babbar godiya ga waɗanda suka karanta wannan jawabi da shawarwarinsu kafin na buga shi. Allah Ya saka da alhairi, Ya biya dukkannin bukatu. Amin.

GABATARWA

A wasu lokatai a tarihin Nigeria, bayan samun mulkin-kai, an yi wasu dattawa masu matuƙar tunani da mutunci da kishin juna da hangen nesa da kishin Kasa. Kodayake sun bambanta a ƙabilunsu da addinansu, amma sun fahimci wani abu guda muhimmi. Wannan abu shi ne: duk runtsi, ba zasu taɓa canja muhallan da Allah Ya halitto su ciki ba. Tilas suka amince, suka zauna tare, suka rayu tare. Haka kuma suka yi fatan dukkannin 'ya'yansu da jikokinsu zasu zauna lafiya da junansu a waɗannan garuruwa da ƙauyuka nasu.

Haƙiƙa kuma, sun fahimci cewar banbamcinsu na ƙabila da na addini, ba su ne suka zaɓarwa kansu ba. Haka Allah Ya yi su. Babu wata gudunmowa da suka bayar, ko wani abu da suka ƙi yi don su kasance yadda suke. Sun san wasu 'yan ƙalilan a cikinsu zasu iya canja addininsu in sun ga dama, amma ba yadda za a yi su iya canja ƙabilarsu, ballantana kuma jinsinsu. Da irin wannan fahimta suka zaɓi su zauna lafiya su

kuma taimakawa junansu, su gina Jiharsu, illa ɗan abinda ba za a rasa ba, daga ibilisan cikinsu.

Waɗannan dattawa masu hankali da kishi su ne shugabanni da sarakunan Arewa na farko. Da:

Musulmansu da Kiristocinsu da Maguzawansu: Akwai Hausawansu da Biron ɗinsu da Barebarinsu da Tivinsu da Fulaninsu da Baburawansu da Jikunawansu da Nufawansu da Igbiransu da Igalansu da Angasawansu da Bachamansu da Yarabawansu da Katafawansu da Idomansu da Dakkarawansu da Bwarinsu da Bolawansu da Badawansu da Kilbawansu da dai sauransu birjik. Amma, abin takaici wasu daga 'ya'yansu da jikokinsu ba haka suka kasance ba a yau, duk da damar da suka samu ta shugabancin al'ummarsu. Ba su kasance masu yakana da gaskiya da kishin juna ba, domin ba su koyi wannan hikimar rayuwa ta aminci ba. Kaico!

Amma dai, akwai kaɗan daga cikin ƙannensu, waɗanda suka shugabanci Jamhuriyya ta biyu, har da kaɗan daga waɗanda suka yi mulkin Soja kafin su da bayansu, waɗanda kuma suka yi ƙoƙarin ci gaba da waccan al'ada ta hankali da

kishi da mutumtaka, suka kuma sami nasara daidai gwargwado, sai dai ba yadda suke so ba. Duk da haka dai an sami ci-gaba a lokutansu.

Amma, ƙoƙarinsu na kafa ƙungiyoyi da kwamitoci don Arewar ba su ɗore ba; kamar yadda wasu abubuwa a Arewar basu ɗore ba. Yawancin ‘shugabannin’ yanzu ta-kansu kawai suke yi. Abubuwan takaici sun faru waɗanda suka cakuɗa al’amura da dangantaka a tsakanin al’umman Arewa. Idan an zauna don a tattauna sai ka tarar 'ƙorafi da zargi' sun fi ‘ya zamu yi' yawa; kuma ko an sami ‘ya zamu yin’, sai kuma aikatawar ta gagara. Daga ƙarshe, siyasu suka shigo suka ƙara rarraba su; wasu suka gaji suka ja da baya; wasu shekaru suka ci ƙarfinsu. Wasu kuma suna nan har yanzu suna tagazawa tareda sababbin hannu a cikin ƙungiyoyi dabam dabam, duk da sunan Arewan.

A yayin da duk wannan abu ke faruwa, sauran ɓangarorin Nigeria suna can suna ta ƙulle-ƙullen yadda za su ci lagon Arewa ta hanyoyi dabam dabam. Da ma dai a mulki kawai muka sha gabansu saboda yawanmu da haɗin kanmu na

lokutan da suka shige. Kuma ma dai, sun amince da mulkin namu, saboda adalcin shugabanninmu, waɗanda tsoron Allansu da tarbiyyarsu, ba su yarda su ci amanar jama'a ba.

Ko da bayan gabatarsu da shuɗewar mulkinsu na Jamhuriyya ta ɗaya, bayan juyin-juya-hali na farko da yaƙin basasar da aka yi, albarkacin mulkinsu ya taimaki Arewa da Kasar sosai a Jamhuriyya ta biyu da bayanta kaɗan. Kai, hattama shugabannin sojan da suka riƙe mulkin Nigeria zamanin yaƙin basasar da ma'aikatan da suka taya su, yawancinsu mutane ne ingantattau, masu kishin Arewar da kuma Kasar baki ɗaya. Ba kasafai zaka ga 'yan Arewa suna nuna bambancin addini ko na ƙabila ko asali a tsakaninsu ba. Arewar, da tunƙaho da ita, su ne rigunan adonsu. Da waɗannan rigunan suka sadaukarda kawunansu suka bautawa wannan Kasa da ƙarfinsu da duk abinda suke da shi.

Amma, tun daga lokacin da 'yan Arewa suka fara juyin mulki a junansu, suna kashe junansu, tun daga sannan ne mutumcin Arewa da kimar mutanenta suka fara zubewa a idanun sauran

'yan Nigeria. Haƙiƙa kam, daga wannan lokaci ne da muka fara nuna ƙiyayya ƙarara ga junanmu, sauran ‘yan-Nigeria suka samu kafar fara renamu. Daga wannan lokaci kuma suka fara tambayar, ‘me ya sa wai su ba zasu yi mulkin nan ba ne?’ Da ma di an ce, “sai bango ya tsage, sannan ƙadangare yake samun kafar shiga”. To yanzu bangon ya kamo hanyar faɗuwa gadan-gadan!

Ba a Nigeria aka fara juyin mulkin soja ba. Fiye da shekaru 200 (a Nov. 9, 1799) da suka shige, Nepolian Banaparte ya fara yinsa a Faransa. Amma su Kanal Gamal Abdul-Nasser ne suka shigo da juyi cikin Afrika shekaru 59 (Juli 23, 1952) da suka shige. Sannan, sai a Kasar Sudan a shekarar 1958. Nigeria ba ta fara nata ba sai a ranar 15 ga Janairu, 1966, yayinda Janar J.T.U. Agui Ironsi ya ƙwace mulki, suka kashe wasu manya a shugabanninmu na farko: Sir Abubakar Tafawa Balewa da Sir Ahmadu Bello (Sardauna) da kuma Cif Samuel Ladoke Akintola da Cif Festus Okotie Eboh. A wannna juyi kuma, manyan sojojinmu irin su Janar Zakariyya Maimalari suka rasa rayukansu. Watau, wannan

Juyin mulki na farko da su Manjo Chukuma Nzeogwu suka yi, haƙon Ibo ne. Ba a daɗe ba ramuwar gayya ta iso daga 'yan Arewa da wasu Yarabawa a ranar 29 ga Juli, 1966. Aka kashe Janar Ironsi da wasu ’yan ƙabilar Ibo; mulki ya koma hannun Leftanan Kanal Yakubu Gowon da abokansa irin su Manjo Murtala Ramat Mohammed da Manjo Theophilus Danjuma; dukkansu 'yan Arewa. Ba a daɗe ba shugabannin ƙabilun Ibo a jagorar Leftanan-Kanal Emeka Odumegu Ojukwu, gwamnan Jihar Kudu-maso Gabashin Nigeria, suka yi iƙirarin kafa tasu Jamhuriyyar ta Biafra a ranar 30 ga Mayu, 1967, cewar sun yanke daga Nigeria tareda duk ƙananan ƙabilun da ke maƙwabtaka da su a Jiha ɗaya. Da sulhu ya gagara a Aburi, Ghana, sai nan da nan yaƙin basasa ya ɓalle a ranar 6 ga Juli, 1967. An mutu da yawa a wannan yaƙin basasa!

Da aka gama yaƙi a ranar 15 ga Janairu, 1970, aka ce an "yafewa" juna, Biafra ta dawo cikin Nigeria, aka sami zaman lafiya aka fara gyare-gyaren Kasa, sai Janar Yakubu Gowon, saboda wasu dalilai, ya jingine alkawarin mayar da

mulki ga farar hula. Wannan, da wasu dalilan dabam, suka sa su Murtala da su Danjuma suka ture shi daga kan mulkin a ranar 29 ga Juli, 1975, yana can wajen taron OAU a Addis Ababa ta Ethiopia. Murtala ya karɓi mulki. Amma bayan watanni bakwai kacal, a ranar Juma'a, 13 ga Fabarairu, 1976, sai su Kanal Sukar Dimka suka far masa suka kashe shi a kan hanya. Haka kuma a Ilorin, suka kashe Kanal Ibrahim Taiwo, gwamnan Kwara. Tunda mafi yawan waɗanda suka shirya wannan kisa daga inda Janar Gowon ya fito suke, sai aka zaci lallai akwai ramuwar gayya a cikin wannan al'amari. Daga sannan sai abubuwa suka fara taɓarɓarewa.

Wannan, a ra'ayina, shi ne ya ƙara zurfafa ƙiyayya tsakanin ƙabilu da addinan 'yan Arewa. Abinda kuma ya biyo baya, ba shakka, daɗa azazzala wannan ƙiyayya ya yi, ya jefata cikin rami wanda ya fi na da zurfi. A shari'ar da aka yi, sojoji fiye da talatin (30) aka harbe. A cikinsu har da Dimkan, da Manjo Janar Bisalla da kuma Kwamishinan 'Yan-sanda, Joseph Gomwalk, gwamnan Jihar Benue-Plateau. Ba makawa, ƙiyayya yanzu ta sami gindin zama. A lokacin,

ba wanda ya hangi abinda zai je ya zo a sakamakon waɗannan ababan takaici.

Da rasuwar Murtala, sai mataimakinsa, Janar Olusegun Obasanjo ya hau kujerar mulki, tareda Birgediya Shehu Musa Yar'adua yana taimaka masa. Waɗannan su suka tafiyarda gwamnatin Soja har zuwa zaɓen 1979 wanda Alhaji Shehu Usman Aliyu Shagari (na NPN) ya ci, ya zama zaɓaɓɓen Shugaban Kasa mai cikakken iko na farko a Nigeria. Tafiyar shekaru huɗu da 'yan watanni huɗu kacal, bayan Shagari ya sake cin zaɓe, sai soja suka sake kai hari a tsakar daren 31 ga Disemba, 1983. Da farko, a watan Yuni suka yi niyyar yin juyin, amma sai suka canja domin kada Cif Obafemi Awolowo ya yi zargin an yi juyin ne don a yi masa ganin ƙyashin cin zaben da za a fara a Agusta, wanda yake zaton shi ne zai cinye. A wannan lokaci, Manjo Janar Ibrahim Badamasi Babangida ne ya shugabanci shiri da aikata juyin, amma kuma ya barwa abokinsa, Manjo Janar Muhamadu Buhari mulkin, ya ce shi ne zai riƙe matsayin babban Hafsan Sojojin Kasa (Chief of Army Staff). A Haka aka tafi. Amma, kafin shekaru biyu kacal,

sai abu ya dagule a tsakanin waɗannan sanannun abokai biyu, saboda wasu dalilai. Kusan daidai da lokacin da Buhari ya yi niyyar kame shi, sai Babangida ya yi wuf ya ture Buhari daga kan mulkin, a juyi na ruwan sanyi wanda ko rauni ba a jiwa wani ba. Wannan kuwa ta faru ne a daren Juma'a, 27 ga Agusta, 1985.

Janar Babangida ya hau mulki da sunan 'President', abu wanda ba a taɓa jin shugabannin Soja sun raɗawa kansu ba; kuma ya fara mulki da sabon salo irin nasa. Tun fari, akwai alamun ya yi la'akari da waccan ƙiyayya da ta shiga tsakanin mutanen Arewa. Wataƙila ma don ya yi maganinta yawancin abokan tafiyarsa na lokacin (waɗanda ake yi masu laƙani da "IBB Boys", watau, 'yaran IBB') mabiya addinin Kirista ne daga langtan; kuma ba shakka su ɗin sun tsaya tareda shi. Amma ga wasunsu, ta ciki na ciki. Babangida kuma, shi ne ya kame abokinsa Dimka, ya yiwa wancan yunƙurin juyi turke, kodayake an riga an kashe Murtala. Sai dai, takaicin kisan da aka yi wa su Janar Bisalla da CP Gomwalk da sauran sojan nan 30, bai fita

daga zuciyar wasu a Arewa ba, kuma haƙiƙa, sun sha alwashin sai sun rama wata rana.

Da farko akwai taɓukawar da wasu suka yi a jagorar abokin Babagidan tun suna yara, watau, Manjo Janar Mamman Vatsa a 1986. Gaba ɗayansu aka kame su aka harbe su, bayan kotun soja (military tribunal) ta same su da laifi. Haka kuma, a ranar 22 ga Aprilu, 1990, sai wasu ƙungiyar sojan, a jagorancin Manjo Gideon Orkar, suka farma Fadar Gwamnati a can cikin 'Barikin Dodan' a Lagos (inda gidan Shugaban Kasa yake), da fushi da kuma niyyar sai sun hallaka kowa a gidan. Amma, cikin ikon Allah, ADC na Babangida ne da wasu ƙalilan suka rasa rayukansu. Janar Babangida da iyalansa duk suka tsira, suka kuma ci-gaba da mulkinsu, suka kame duk 'yan tawayen, suka sa su a Kotun Soja aka harbe su. Ba shakka, wannan ma ta daɗa zafafa ƙiyayya tsakanin ƙabilun, wadda kuma ta fara zama ta addini. Amma, har yanzu akwai masoya a cikinsu waɗanda suke ganin "Arewancin" yana da muhimmancin gaske wajen ɗinke dangantaka a tsakanin addinan da ƙabilun Arewa.

A haka dai, President Babangida ya ci gaba da mulki, kuma bayan 'yan watanni ya yi alkawarin sakin 'yancin siyasa ta hanyar kafa jam'iyyu da shirya zaɓe da niyyar maida mulki ga 'yan siyasa. Wannan ita ta kaimu har zuwa zaɓen da aka yi a ranar 12 ga Yuni, 1993, wanda aka soke. Wannan sokewa tana da nata mushkilolin.

Daga ƙarshen rigingimu iri iri, a sakamakon soke wannan zaɓe, waɗanda suka tada hankalin kowa, sai President Babangida ya sauka daga mulki, a ranar 27 ga Agusta, 1993, ya miƙa mulkin ga wani abokinsu, ɗan-kasuwa (kuma shugaban kamfanin UAC) ɗan Jihar Ogun, Cif Earnest Shonekan. Amma kuma ya bar ɗaya abokin nasa, Janar Sani Abacha (wanda tare suka yi ta yin waɗancan juye-juyen mulkin), yana riƙe da muƙamin Ministan Ma'aikatar Soja da tallafin ɗaya abokin nasa, Janar Aliyu Gusau a matsayin hafsan hafsoshin rundunar Soja. Su ukun nan, tun farkon shigarsu Soja suke tare. Haka kowa ya gansu, haka kowa ya sansu.

Janar Sani Abacha da Janar Aliyu Gusau, su ne suka tsorata Cif Shonekan, suka karɓe mulkin

daga hannunsa. Dayake shi dattijo ne mara son rigima, sai ya rufawa kansa asiri ya hanzarta ya koma gida a Abeakuta. Wa zai shiga tsakanin Soja? Amma, wasu sun ce da ma can ya san da shirin. Toh, ko hakane, ko ba haka ba ne, marubuta tarihi zasu bincika nan gaba.

Janar Sani Abacha ya karɓa ya ci gaba da mulkinsa yadda yake so da irin nasa shirye-shiryen, har dai tasu da Janar Aliyu Gusau ita ma ta daki bango. Toh, amma, akwai wani ɗan Abeakutan wanda bai yarda da abubuwanda ke faruwa ba, kuma yana ganin shi shugabansu ne duka a da can. Wannan shi ne tsohon Shugaban Kasa, Janar Obasanjo. Da ya fara surutai da ganin damarsu, sai Abacha ya cafke shi tareda da Shehu Yar'adua ya jefa su a kurkuku da zargin suna shirya juyin mulki. Haka kuma ya yiwa mataimakinsa, Leftanan Janar Oladipo Diya, da irinsu Manjo Janar Abdulkarim Adisa na Kwara. Sauran labari dai kowa ya sani har zuwa yau.

Kodayake a can baya ma, fushi da juna saboda saɓanin ra'ayi sun taɓa tunkuɗa 'yan-Arewa rabuwa cikin Jam'iyyun NPC da UMBC da

BYM (Borno Youth Movement) da NEPU da sauransu, amma a wannan tarihi na kurkusa, ba shakka yawan juyin mulki bayan juyi, shi ne muhimmi, a ganina, na dasa sabuwar ƙiyayya tsakanin ɓangarorin Arewa. Lokacin da su Gowon, su Ɗanjuman, su Bisallan, su Murtalan da su Ibrahim Taiwon suka durfafi su Agui Ironzin, sun yi tare ne da sunan su 'yan-Arewa ne. Kuma kada mu manta, dá suna tunanin ƙabilanci ko addini a zuciyoyinsu lokacin da suka haɗu suka ture Janar Gowon, da ba su yi wannan juyi ba, saboda sun bambanta a waɗannan abubuwa.

Toh, amma da aka shiga juye-juye da lahanta juna a sakamakon haka, sai dangantaka ta fara ɓaci. Kuma a hankali, tunda babu wanda ya yi ƙoƙarin sulhuntawa, don ma ba wanda ya fahimceta sosai, wannan ƙiyayya ta yi zurfin da ta tashi ta riƙa ta sa rigar addini.

A fahimtar wasu al'umman Arewan, sun rasa wasu guraba ne; ko kuma an caje su ne daga mu'amullolin mulki da tattalin arziki; ko kuma an ƙasƙantarda su ne saboda bambancin ƙabila

da addini, kuma suna zargin wasu ‘yan-Arewan ne dabam suka jawo masu. Ba shakka, duk ta’annatan da muke ta yiwa juna har zuwa yau, a wasu jihohin Arewa, ɓurbushin wannan ƙiyayya ce da ta kafu tuntuni, wadda rashin shugabanci a Arewan ya barta ta yi yaɗo.

Yanzu, mun fahimci wasu abubuwa mihimmai na tarihi daga yadda muka yi ta yi wa juna taɓargaza, har sai da daga ƙarshe muka rasa ɗan mulkin da muke taƙama da shi a wannan Kasa. A haka da haka, aka zo lokacin zaɓen da aka yi a ranar 12 ga Yuni, 1993, wanda aka soke saboda wasu dalilai. Wannan soke zaɓe shi ya kawo Shonekan, ya kuma sake kawo Obasanjo. Haƙiƙa, yana da nasa muhimman nauyin ga Arewa musammam, da kuma Kasar gaba ɗayanta.

Ko da ’yan-Arewa suka fito da Janar Obasanjo daga kurkuku a zamanin Janar Abdussalami Abubakar, suka sake miƙa mulkin Nigeria gareshi ta hanyar zaɓen da har yanzu ba a fahimci gaskiyarsa ba, haƙiƙa ba su yi la’akari da yanayin zuciyarsa na fushi da ƙudurin sai ya

yi ramuwar gayya a kan Arewa gaba-ɗayanta ba. Fushin cin zarafin da wasu suka yi masa, a gunsa, ya fi girmamawar da Arewan ta yi masa na sake miƙa mulki a hannunsa a karo na biyu. Masu mahawarar tarihi suka ce, ai 'yan-Arewa sun amince masa ne ganin yadda ya dage a kan gaskiya, ya tabbatar da an ba wa Alhaji Shehu Shagari nasararsa a zaɓen 1979, duk da cewar Cif Obafemi Awolowo bai amince da hakan ba. Shari'ar da aka yi wata magana ce dabam.

Masu nazari, harwayau, sun ce ƙudirinsa ne ya yi ramuwar gayyar kurkukun da Janar Abacha ya jefa shi ciki, ta hanyar illata Arewa da kuma shirya makircin da zata daɗe ba ta sansana mulkin Kasar nan ba. Don hakane ma ya yi kutun-kutun ɗora ƙanin abokinsa, Umaru Musa 'Yar-Adua, wanda lafiya ta gaza masa, kuma wai lokitoci sun yi zaton cutar ta ajali ce! Watau, manufar ita ce, Umaru yana rasuwa sai kawai su kawo ɗan-Kudu su ɗora a kan mulkin. Toh, ko hakan ne, ko ba hakan ba ne, hakan dai ce ta faru; aka kuma ɗora mataimakinsa, Goodluck Ebele Jonathan, ɗan Kudu-maso Kudu a kujerar

shugabancin Nigeria. Allah Ya jiƙan Shugaba Umaru, Ya gafarta masa. Amin.

LALACEWAR AL'AMURA

Bayan rasuwar Shugaba Umaru Musa Yar-Aduwa, sai siyasar Arewa ta sake yiwa kanta jina-jina; abu wanda ya haddasa hasarori iri iri. Wasu kaɗan suka ci girma suka haƙura, amma sauran suka kasa haɗa kawunansu saboda wasu dalilai. Daga ƙarshe duk aka rasa. Wannan, ba shakka, laifinmu ne 'yan-siyasa da kuma waɗanda suka shigo saboda kwaɗayin mulki. Sannan akwai 'yan ci-da-siyasa da suka butulci mutumcinsu suka tsallaka katanga don kwaɗayi, suka koma bayan waɗanda suke zagi a da. Ba shakka, wasu 'yan Arewa kam sun lalace. Ba tarbiyar da shugabannin farko suka koyar ba kenan. Abin kunya! Irin waɗannan mutane masu kwaɗayi da rashin mutumci suna cikin manyan jidalanmu a Arewa. Yawancinsu an sansu; kuma har yanzu suna nan! In dai suka ga kuɗi,

hankalinsu ba zai dawo masu ba, sai sun kai ga kuɗin nan. Wannan maita!

Wasu masu hikimar magana, sun taɓa cewa, 'yan Arewa “mulki” suka iya; 'yan Gabas “kasuwanci”; 'yan Yamma kuma “aikin Gwamnati da na Banki”. Toh, in hakane, su 'yan Gabas ɗin sun yi amfani da Kasuwancin sun handame ciniki da hanyoyin arzikin Kasar nan, sun gyara kansu da rayuwarsu ta ɓangarori da dama. Haka, su ma 'yan Yammar, sun yi amfani da muƙamansu, sun gina kansu sosai, sun kuma yi saitin makomarsu yadda suke so. Ko siyasarsu ka auna, zaka fahimci mafi yawancinsu don amfanin jihohinsu da ƙabilunsu suke yinta. Wanene zai soke su a wannan? Sai ka ji ana cewa 'Yarabawa sun faye son kansu. Kabilancinsu ya faye yawa!' Haka za a faɗawa Ibo: ‘Kai! Inyamurai? Ai sai kansu kawai suka sani'. Toh, wa ye ya yi sakaci a cikinku? Ina naka ɗabi’un suka kai ka tareda al’ummarka? Me ya sa kai ba zaka kare kanka, ka kuma so wasun don a sami daidaito ba?

Mu, ba kasafai muke son taimakon kanmu ba. Ko wata harka ce ta bijiro, mun fi son mu yi da wasu can, wai don kada a gane mu! Yanzu, ma'aikatan Gwamnati da 'yan-kanzaginsu su ne masu kuɗi, amma ba 'yan-kasuwa ba, kodayake duk haka Kasar take. Manyan ma'aikata da zaɓaɓɓu da naɗaɗɗu kamfanoni gare su.

Haƙiƙa, ɗabi'ar ƙabilanci ba zata taimaki Kasa gaba ɗaya ba. Toh, amma, idan ana yi maka shi, lallai ne ka tashi tsaye ka gyara, ka kuma nemi yadda zaka kare kanka ka nemi haƙƙinka, ba tareda kai ka yi ƙabilancin ba. Yin haka kuwa, sai ka kare mutumcinka tun farko.

A zamanin da wannan sabuwar ƙiyayyar ba ta riga ta dasu a tsakanin al'ummun Arewa ba, su ne riƙe da mulkin Nigeria fiye da kowanne sashe na Kasar nan a cikin tarihinta, tareda alfahari da ƙoƙarin yin adalci ga kowanne ɗan Nigeria. Sai dai kuma ba mu yi amfani da "mulkin" mun ci ƙarfin mushkilolinmu ba, kamar yadda su suka yi amfani da mu da kasuwancin da aikin gwamnatin nasu suka gyara yawancin al'amuransu, ballantana kuma yanzu da suke

mulkin. Dalilin ba wai don waɗanda suka yi mulkin a da ba su da kishin Arewan ba ne. A a. Sai dai kawai don irin wannan son-kan da rashin sanin yakamatan ba sa cikin ɗabi'unmu.

Kodayake dukkannin waɗanda suka yi mulkin daga Arewan sun ɗan hango nesan, kuma sun taɓuka, amma kawaici da gudun zargi ya sa ba su tunkari ko hanzarta wasu abubuwa ba. Alal-haƙiƙa, a waɗannan lokuta, giyar mulki ta ɗan bugar da wasu 'yan-Arewa yadda hangenmu gaba ɗaya ya zama dishi-dishin da ba ma ganin gabanmu sosai. Sannan kuma ga 'yan-ɓace daga wasu gurare, da munafukai da makwaɗaita da yawa. Amma kuma, ba lokacin da Arewa ta yi babbar hasara irin daga shekarar 1999 zuwa wannan lokaci!

A waɗancan lokuta na baya, da mulkin Kasar nan yake hannunmu, 'yan shagwaɓa ya maida yawancinmu. Yanzu kuma da mulkin ya kuɓuce mana, sai ga shi kwaɗayin 'yan Arewa bai gaza na muƙaman da suke riƙewa, ko na abubuwanda suke nema a gwamnati ba. Tun kafin 1999, 'Yan Kudun da suka yi mulki, ko suke yinsa a yanzu,

tuni sun fahimci 'yan Arewa da wannan hali na lalaci da son banza. Haka kuma sun san duk tsananin wulaƙanci wasu 'yan Arewa ba za su taɓa ƙurun bijircewa Shugaba ba muddin dai za a barsu su ci moriyar muƙamansu don kansu ba don Arewan da Kasar ba. In ba haka ba ne, me yasa suna cikin gwamnatin ake tsaida shawarwarin da zasu ƙwari Arewan, ko ma wani sashen, amma ba sa iya magana?

Harwayau, kuma hassada da ganin-ƙyashin juna sun sami gurbi a Arewa; yadda ba kasafai muke son ci-gaban junanmu ba. Sannan ga mu da son nuna wani bai isa ba. Sai ka ji an ce, "ai Arna ne". Ba su san Kirista ba arna ba ne. Arna, a Hausa, su ne waɗanda ba su da addini. Ko kuma ka ji an ce, “waye ubansa?” Ko musulmi ya maƙalawa ɗan'uwansa kafirci kamar an aiko shi da iznin yin hisabi. Kuma in ka bibiya duk don wani abu da za a samu, ko ake ganin za a rasa in ba a aiwatar da waɗannan miyagun halaye da maganganu ba. Sannan ga tsagwaron jahiltar addinan su kansu. Mafi munanci, an bar Allah; sai zunubai tsagwaro ba kunya. Tsafi, luwaɗi, maɗigo, ƙarya, munafurci, sata, rashin gaskiya

da sauransu sun yi yawa a Kasar nan gaba ɗayanta. Waɗannan illoli sun ci ƙarfin mutane da yawa; kuma lallai a san bala'ai ne ga Kasa.

Wani abin takaici kuma shi ne, mu yi ta kashe kanmu, muna yi wa juna ɓarnar dukiya, saboda mu Musulmai ne ko mu Kirista ne! Mun manta da cewar har a naɗe Kasa a tare zamu zauna; a gari ɗaya ko ƙauye ɗaya. Mu sha ruwa daga famfo ko rijiya ɗaya; mu hau tituna ɗaya, mu je kasuwa ɗaya; 'ya'yanmu su je makarantu ɗaya da sauransu. A Arewa, ko ma a Nigeriyar, ba za a daina ganin Musulmai ba. Ba za a daina ganin Kirista ba. Lallai ne mu yi tunani saboda Allah a kan wannan!

Al'amura a Kasar nan sun dagule fiye da yadda wasunmu da yawa zasu iya jurewa. Rashin gaskiya da yawan sace-sace a gwamnati sun kai maƙura; sun sa talauci ya bazo Kasar gaba ɗaya. Waɗanda ba ruwansu, an bi su an tsokane su; wasu an kashe; wasu kuma an barsu su mutu da yunwa da cutuka. Haƙiƙa, adalci ya kau a wannan Kasa tamu. Lallai ne mu san ba addinanmu ne maƙiyanmu ba. Waɗanda suke

talauta mu, suke amfani da mu don biyan bukatunsu, su ne maƙiyanmu. Rashin zaman lafiyar shi ne ribarsu; mu kuma hasararmu.

Yanzu ya zama wajibi mu zauna da junanmu, a cikin unguwanninmu da ƙauyukanmu, da biranemu, mu tattauna mu samo maslahar da zata amfanemu. Haƙiƙa, rashin shugabanci da rashin sanin yakamata a al'umma sun gallabe mu. Idan shugabanni suka ci gaba da shagala, suna gani ana aikata irin wannan taɓargaza ana illata wasu ba su hana ba, toh su kansu zasu yi danasani wataran. Shugabanni a matakai da yawa sun zura ido, har yanzu ko uffan ba su taɓa cewa ba.

Ko me ya sa?

Toh, fatanmu dai shi ne, waɗannan shugabanni su farka su gyara kura-kuransu. Babbar hanya ɗaya ta yin haka, shi ne su tsaya tsayin daka su tabbata an aiwatarda irin shawarwarin da na bayar a shafunan gaba (sh.35-38).

SASHI NA BIYU

ZUBEWAR MUTUMCI

A gaskiya, duk wanda ya nutsu ya auna al'amura ba tareda tsoro ba, zai tarar da cewar mutanen Arewa su ne babbar mushkilar kansu ba wasu ba. Lallai mu daina ɗorawa wasu dabam nauyi ko laifin jidalanmu. Mu ne muka rena kanmu har sai da alkadarinmu ya karye ya fara ruɓewa. Duk wanda bai kare mutumcinsa da na wasu ba, ko kuma ya ƙaskantarda kansa don kwaɗayin wani abu na duniya, toh ba shakka sai ya ga wulakanci. Bai mai wulakantaka sai ka yarda. Na farko kenan.

Na biyu kuma, a nan Arewa, sakaci da son banza da lalaci sun yi kaka-gida. Kuma ba gwani a cikin jama'a sai mai kuɗi. Ba wanda ake tsoro sai shaƙiyyi da mara kunya. Ba wanda ake yabo da girmamawa sai ɓarawo. Yawancin jama'a ba ruwansu da gaskiyarka ko ɗa'arka, ko tsoron Allanka, in baka da kuɗin da zaka ba su. Ashsha! Wannan lalacewa da yawa take!

Kuma, wannan illa ta fi yawa a cikin musulman duk da shiriyar da addininsu ya koyar. Haƙiƙa, wasunmu da yawa, musulunci da kiristanci ba addinansu ba ne; al'adunsu ne kawai. Haka dai suka tashi suka ga ana yinsu, su ma suke yi.

Na uku: Zumuncin da aka sanmu da shi a nan Arewa, musammam na maƙwabta 'yan-unguwa ɗaya, da na 'yan'uwantaka, da kuma na 'yan-Arewancin, yanzu ya ragu ta yadda in ka ganshi ma da kyar zaka shaida shi. Lallai mu yi tunani sosai a kan wannan zagwanyewar zumunci namu. Da can ba haka muke ba. Me ya faru?

Dá mã zancen kishi babu shi. Ko a bakan ma ya ragu. Haka zancen tunanin wakilci nagari babu shi. Kowanne nawurezu sai ya tsaya zaɓe a inda ma ba a san shi ba, a kuma zaɓe shi, ba wanda ya damu da tarihinsa ko ƙwazonsa, ballantana gaskiyarsa da dacewarsa; ko ma kasancewarsa ɗan gurin. In dai ya kai 'gaisuwa' ga manya, ko ya raba kuɗi ga talakawa, toh shi ne wanda ya cancanta. Da wannan lasisin, shi kuma zai tafi ya shiga tasa ɓarnar. Me zaka iya cewa? Ya riga ya ba ka kamashonka. In talauci zai kasheka, sai dai

ya kalle ka ya yi dariya. Ya san kai lusari ne. Idan ma wataran ya sa aka dakeka ya yi daidai a ganinsa, domin kuwa ya san kowaye kai. Kuma ba wani abin kirki da zai ƙulla maka a majalisar in ya je, sai baƙin ciki.

Haka kuma, tausayi da taimako da kula da juna yanzu sun kau, ballantana kuma a ce ya zamu yi da yaran nan masu kangarewa? Muna ganinsu suna shan ƙwaya, suna daba da sauran miyagun ɗabi'u, amma ko zancen ba ma yi da gaske, ballantana mu yi wani abu a kai. Ba ilimi ba aikin yi! Waɗannan yara da samari su ne fa manyan gobe; kuma goben nan ta fara isowa. Ita ce saukar bala'i iri iri a jihohinmu na Arewa. Lallai ne mu san cewar wannan ba ƙaramar masifa ce ba a garemu.

Na yi imani, idan muka bar wannan ta faru, nadama ita ce ƙaramar juyayinmu! Lallai shugabanni su yi wani abu a kai cikin gaggawa. Na sha ba da shawarwari waɗanda zasu taimaka mana wajen neman maganin yawancin waɗannan matsaloli waɗanda iskarsu ta fara busowa. Amma, duk lokacinda na yi magana, ko

na rubuta na rarraba, ko na kira taro aka fara tattaunawa, kafin a je ko'ina an watsar. Da mã, wani ya taɓa ce min, "kome ka zo da shi an yarda, amma kai za a bari da shi". Mutanenmu ba sa son aikin wahala. Allah Ya sa samari masu tasowa ba zasu koyi wannan hali ba. Lallai su yi la'akari, su kuma tashi tsaye su fara tunanin yadda zasu taimaki kansu da kansu.

Mutanen Arewa sun zubarda arzikinsu, saboda lalaci da son su ci bulus. Yawancin mutanenmu ba sa son su yi wani yunƙuri mai wahala domin su rufawa kansu asiri. Sun fi ganin sauƙin roƙo ko bara, ko su ɗorawa wasu abokai ko 'yan'uwa nauyin rayuwarsu. Sannan ga wani rashin tunani: Sai ka ga ɗan shekara 60 ko ma fin haka, har yanzu yana ta aurace aurace. Da ka yi magana sai ya ce, 'bakin da Allah Ya tsaga...' Ko yaushe shi zai fara tasa rayuwar? Ko waye zai kular masa da su in baya nan? Addinanmu sun hore mu da mu yi wa 'ya'yanmu tarbiyya, amma ina! Lallai mu bar waɗannan guragun al'adu a baya, mu san 'ƙarko' ya fi 'yawan' banza. Ɗanka ɗaya ƙwaƙƙwara ya fi haihuwa yuyuyu alhairi.

Karancin Ilimi da kantar talauci tuntuni suka fara addabarmu a nan Arewa. Mutane suna ji suna gani suna ta talaucewa. Jari yana zagwanyewa. Kowa ka tambaya, sai ya ce, “jiya ta fi yau!” Wannan abin damuwa ne.

Mun kasa tattara hankulanmu wajen yadda zamu cicciɓi juna domin mu inganta makaman tattalin arzikin da Allah (swt) Ya ba mu. Ga shi yanzu Arewan ba ta da komai nata. Da Masana’antu da Bankuna da Ciniki da Jari da sauransu duk sun yi wasu gurare. Kodayake Gwamnoninmu suna yin taro a kai a kai domin su duba abinda Arewan take ciki, amma kuma har yanzu sun kasa haɗa gwiwowinsu domin su yi wasu abubuwa muhimmai tare waɗanda zasu amfani Arewan gaba ɗaya. ‘Yan-kasuwanmu da yawa ba ruwansu da juna; ba amana sai hassada. Yawancinsu ba sa son gina masana’antu sai dai su rufe su. Sun gwammace su zama dillalan wasu; ba sa tunanin abinda zai je ya zo. Ranar da masu ba su kayan suka hanasu, rannan zasu fara yin da-na-sani. Gara a farka tun yanzu.

Ko Gidauniya aka kafa da niyya kyakkyawa, iyakacinta wannan bukin. Haka ƙungiyoyi zasu yi ta yin taro kamar gaske, amma duk a banza, domin daga ƙarshe sai ka tarar wasu ne suke son su yi amfani da wasu domin biyan bukatunsu. Ko wasu su lalata taron. Ko kuma duk a janye a bar wasu da wahalun, har sai su ma sun gaji sun watsar. Gaba ɗaya an yi babbar hasara, amma ba a koyi darasi ba.

A siyasance mun zama maƙiyan juna, mun kasa gudanarda tunaninmu da adawarmu yadda zasu amfane mu. Sai dai mu yi ta yin hassada da illata juna. Mun fi tuna sharrin da muka ji ko muka gani, maimakon alhairan. Gasar neman shugabanci da na muƙaman gwamnnati sun zama sanadin yaƙin juna; kowa ya ja dabur ba mai son ya bar wa wani. Gara wani can ma ya yi da naka ya yi, don baƙin ciki ga juna.

Ban faɗi waɗannan abubuwa don ban ga wani abu mai kyau a garemu ba. Akwai mutane da yawa nagari, masu kishi da riƙon amana birjik a Arewa a cikin musulman da kiristocin; haka kuma a cikin ƙabilun. Amma, kaico! Ba irinsu

muke nema ba. Da sun yunƙuro don kansu, sai mu buge su mu ce basu isa ba; ko kuma su tarar abin sai masu kuɗin saya.

A jihohin Kudu, in sun san kai ka dace da abu kaza, toh sai sun matsanta maka, ko sun biya maka, ko sun taimaka ka zama wannan abin don ci gabansu gaba ɗaya. Amma a Arewa, ko wasu sun ambaceka, sai wasu sun kushe ka, kuma ba wani dalili sai hassada da ganin ƙyashi. Ko wani abu ka fara yi don ci gaban jama'a, sai wasu marasa tunani, waɗanda su basa yin komai, sun ce wai wani tsari naka na kanka kake da shi; ko su ce ai shugabanci kake nema. Wannan takan sa mutanen kirki su ja da baya su zura ido. Duk sa'inda haka ta faru, hasarar al'umma ce gaba ɗaya, ba ta mai son taimakawar ba ce shi kaɗai. Amma ba a yi la’akari ba.

A Arewa, wasu masu hali da masu riƙe da muƙaman Gwamnati (ban ce duka ba) kansu kawai suka sani. Wasu, babbar manufarsu su je su yi tasu ta’asar. Sai ka ji an ce, Alhaji 'Wane’ ne Ministan Noma. Amma ba abinda zaka gani an yi da zai haɓɓaka ayyukan noman a Arewa,

ko ma a Kasar. Sai ma ka tarar a kasafin kuɗi na shekara, kaso 3 cikin 100 kacal aka warewa komai na noman a Kasar gaba ɗayanta, amma ba zai iya yin magana ba. Shi abinda ke gabansa ya ba da kwangilar sayen taki ya kwashe 'yan kan. Ko a ce, 'Mista Wane' ne Ministan Ayyuka, amma ko ɗan titin zuwa garinsu ba zai gina ba; shi dai ya sa hannu a babbar kwangila a ko ina ne Mista President ya umarta, don ta kamashon da zai samu kawai yake yi. Duk abinda Mista President ya ce masa, sai ya ce, “hakane, ranka ya daɗe”, wai don kada ya kawo wani hanzari dabam a kore shi. Akwai ’yan ƙalilan na kirki masu kishin Arewar da Kasar, sai dai an fi ƙarfinsu!

Haka wasu mutanenmu suke. Ka gansu manya manya kamar gaske. Amma Ina! Ta kansu kawai suke yi. Da yawa a cikin manyan sarakuna da manyan malamai da manyan 'yan siyasa, sauraron me za a basu suke yi, basu damu da wanda zai basun ba, ballantana a ina ya samo abinda yake basun. Lallai ne shugabanninmu da iyayenmu su san yadda suka dawo da mutuncinsu da darajarsu; su shige gaba wajen

gyara al'amuranmu, kamar yadda aka sansu da can. Yanzu ma zasu iya.

Duk waɗannan halaye ba zasu canju ba, sai mun zauna mun faɗawa kanmu gaskiya, mun kuma kama hanyar gyarasu gadan-gadan. Allah (swt) Ya ce ba zai gyara halayyar ɗan-Adam ba, sai shi ɗan-Adam ɗin ya gyara tunaninsa da kansa. Haka Ya sake cewa, duk abinda ya sameka mai kyau, Shi ne. Amma duk abinda da ya sameka marar kyau, toh kai ne ka jawowa kanka. Allah Bai yarda a jingina munanan abubuwa da Shi ba. Amma duk katoɓarar da muka yi, sai mu ce, 'haka Allah Ya yi.' Babu muguwar al'ada irin ka ƙagawa Allah abinda ka jawowa kanka. Kuma haka duk yawancinmu muke, musulmanmu da kiristanmu.

Saboda haka, mu kwanta muna shashanci, wasu ma da izgilanci, muna cewa Allah Ya gyara, ko Ya sawwaƙe, toh ba Zai gyara ba; ba Zai sawwaƙe ba. A duniyar nan tamu, shiriyar ita ce: iya tsari da kwazon fafutuka ta gaskiya su ne kaɗai jagorar addu'a. Idan har ba ka yi waɗannan ba, addu'arka ba ta ginu a kan tushe

mai ƙarfi ba. Ko a yarda ko kar a yarda, haka abin yake. Yardar ita ce makarin imani.

Amma, idan muka tashi da gaske da kuma gaskiya da nufin alhairi a zukatanmu don mu gyara al'amuranmu da junanmu, don mu samo maslahohin mushkilolinmu; sannan muka nemi taimakon Allah, toh ba shakka Zai taimaka cikin gaggawa ta irin hanyoyin alhairin da ba ma zato.

*****

SHAWARWARI:

Ya zama wajibi ga dukkaninmu, 'yan-Arewa, mu yarda cewa zaman sulhu da shawara da juna ya zama tilas a garemu, cikin matuƙar gaggawa, saboda lokacinmu ƙurarre ne. Idan ba mu tashi mun yi da gaske ba, mun ha'inci kanmu.

Zai dace kowacce Jiha ta Arewa, a jagorancin Gwamnoninsu da manyan Sarakuna da manyan Limamansu na Kirista da Musulmai da manyan 'yan-Siyasarsu da manyan Tajiransu da wakilan Samarinsu da Mata, duk a zauna a wani babban taron da yakamata mu yi, domin:

1. Mu faɗawa kanmu gaskiya. Mu tsageta, mu kuma karɓi laifukan da muka yi wa juna; sannan mu yafewa juna saboda Allah. Ba wani musu, ko ka ce-na ce a wannan guri. Watau, wannan zaman sulhuntawa ne kawai. A yi kwana uku ko fin haka ana yinsa a inda ake ganin ya fi dacewa.

2. Mu tattauna dangantakar da ke tsakaninmu da irin yadda zamu zauna lafiya da juna; da ƙa'idoji da haƙƙoƙin da zamu kiyaye a tsakanin juna; da yadda zamu zama 'yan'uwa mataimakan juna. Sannan mu tabbatarda yarjejeniyar da zata ɗinke mu gaba ɗaya cikin daidaituwa da kishin juna.

3. Mu yi nazarin halayyanmu da yadda zamu yi maganin duk illolin da suka bazu suke kuma gurɓata mana rayuwarmu.

4. Mu yarda da muhimamncin waɗannan addinai namu biyu, na Musulunci da na Kiristanci ga mabiyansu; mu ja marasa addini a cikinmu, sannan mu san yadda

zamu kiyaye tsokanar juna ta kowaɗanne irin hanyoyin tsokana. Mu sa ƙa'idojin Da'awah da Wa’azi; mu kuma yawaita ziyartar bukukuwan juna da suka dace.

5. Idan wannan ta samu, sai a yi wani shirin wanda za a gayyaci masana da masu hikima, domin:

a. Mu binciki duk irin arzukan da Allah Ya yi mana a Arewa, waɗanda suke binne a ƙarƙashin ƙasa da waɗanda suke a doron ƙasa da waɗanda suke ga yawan al'ummarmu; mu san yadda zamu sarrafa arzikin don amfanin mutanenmu da Ƙasar baki ɗaya. Haka, zamu duba hanyoyin zuba jari da yadda zamu iya inganta haɗin gwiwa.

b. Mu auna siyasarmu da siyasunmu domin mu sami mafitar da zata kaimu ga yalwatar alhairi ga dukkaninmu gaba ɗaya; wadda zata tabbatar mana da zaman lafiya a junanmu da sauran jama’ar Ƙasar nan.

c. Sannan mu duba yadda zamu kawo maslaha ga dukkannin abubuwan da suka dami al'ummarmu, dagane da talauci da jahilci da cutuka da gangare war samari da yadda za a taimaka masu ta fannin ilimi da sana’o’i da ayyukan yi don rayuwarsu ta inganta; kuma bayanmu ta yi kyau.

d. Lallai ne kuma mu koma sosai ga Allah.

Na yi tunani mai zurfi a kan wannan al'amari, kuma na yi ƙoƙarin yin wani abu a kai. Abinda nake ganin yakamata a yi shi ne: a sami mutane goma (musulmai biyar, kirista 5), 'yan-Arewa masu mutumci, kuma yardaddu ga yawancin jama'a, su zagaya dukkannin Jihohin nan 19 na Arewa, su ziyarci duk waɗanda yakamata a kowacce Jiha, su yi masu cikakken bayani gameda haɗarin da Arewa take ciki. Sannan su ja hankalinsu wajen mahimmancin a yi taron. Su waɗannan mutane goma, su kuma shirya komai na taron da taimakon waɗanda suka ga ya dace su taimaka.

Idan kuma hakan ba zata samu ba, toh sai wasu masu kishin Arewar (a cikin ƙungiyoyi, ko a gaurayen musulmai da kiristoci masu son a haɗa-kai a zauna lafiya) su ɗau wannan nauyi, su zagaya Arewar da kansu su ja hankulan jama'a, sannan su shirya taron.

Yin wannan ya zama tilas, kafin mu faɗa rami.

SASHI NA UKU

AREWA A NIGERIA

Tunda farkon fari, lallai ne na jaddada mana muhimmancin kasancewar Nigeria Kasa ɗaya. Haka kuma, wajibi ne na ce, idan ba Arewa a Nigeria, ba Nigeria, domin Arewa ce ginshiƙin kasancewar Nigeria Kasa ɗaya. Duk wahalhalun da miskilolin da Arewa take ciki a halin yanzu, rashin tasamma gyara su da gaske, ba ƙaramar hasara yake jawowa Nigeria ba. Ra'ayina ne cewar Arzikin kowanne sashi na Kasar nan, ribar dukkanninmu ce gaba ɗaya. Haka, talaucin kowanne sashi na Kasar nan hasararmu ce gaba ɗaya. Duk mai hankali da kishin Kasar haka zai ce maka.

Arewa a zahiri, ita ce kaɗai mafakar duk 'yan Nigeria ba tareda tsangwama matsananciya ba. Wannan, ba ƙaramin ginshiƙi ba ne ga wannan Kasa tamu. A nan Arewa ne kaɗai kowanne irin ɗan Nigeria yake miƙe ƙafarsa ya yi abinda ya ga dama, fiye ma da yadda zai yi a inda ya fito tun asali. Kodayake, duk wannan 'yanci da 'yan

Nigeria suke da shi a Arewa abin alfahari ne a garemu (mu ‘yan Arewan), amma idan talauci ya fara cin ƙarfin 'yan Arewan a Arewa, toh kuwa ba shakka, kada a yi mamakin taɓarɓarewar dangantaka. Wannan kuma na iya jawo babbar tarzoma nan gaba. Saboda haka, talaucin ‘yan Arewa, ba abin dariya ba ne ga ‘yan-Kudu. Su sani cewar, zaman lafiyarsu da bunƙasarsu duk sun dogare ne a kan samuwar ilimi da koruwar talauci a Arewa da Kasar. In suna da wani tunani dabam, toh babban nazari ya same su.

Wani abin takaici shi ne irin abubuwan da muke ta karantawa a ‘yanar gizo’ (internet) da jaridu da mujallu daga wasu 'yan-Kudu, suna yi wa Arewa habaici, har da barazanar kora daga wannan Kasa tamu. Tun suna yi a sirrace, yanzu ta kai a fili suke yi, kuma hukuma ba ta kula su ba. Shekara da shekaru suna ta zancen wai kowa ya riƙe abinda ya yake da shi na arziki (watau, **'resource control'**). Ina tabbatar masu duk waɗannan zantattuka na rashin kishin Kasa, ba ƙaramin sharri ne garesu ba. Yawan arzikin da yake a Arewa ba kaɗan ba ne. Ya ninka na Kudu ninkin ba ninkin, aƙalla. A cikin arzikin Arewa

makoma da zaman lafiyar Nigeria suke nan gaba, lokacin da Man ya ƙare, ko aka kasa haƙo shi saboda wasu dalilai. Bincike ya tabbatar da haka. Masu son ji, ko ganin ƙwaƙwaf sa iya tonawa.

Idan aka ce kowa ya ci gashin kansa kawai toh, ba shakka, wannan zata jefa Arewa cikin wahalu na ‘yan shekaru 3 zuwa 5 ne kacal, kafin ta miƙe ƙafarta cikin arzikinta na kanta. Amma a can, da wuya su yi rayuwar kwanciyar hankali, ballantana su ci arzikin ‘Man’ da suke taƙama da shi, in ma sun zauna tare. Don hakama tun farko na ce, ‘in ba Arewa, ba Nigeria’. Muna sane da irin zaman ‘doya da manjan’ da suke yi, kuma mun san irin ƙiyayyar da ta yi kanta a tsakaninsu, wadda Arewar ta kwantar. Kuma, su yi tunanin tsarin Kasar ba Arewa, su ga yaya zasu yi, ko da a Kudu-maso-Kudun?

A Arewa, ko faɗi da sararin Kasa da yalwar iska da zafin Ranar da muke da su, muka ce zamu riƙe don amfanin kanmu kaɗai, a ina milyoyinsu zasu sa kansu? Haka kuma, abin takaici, sun manta cewar

kusan yawancin ɗan abinda muke samu daga kasafin kuɗin shigowar, da su muke rabawa saboda yawan mutanensu a nan Arewan. Su sha Ruwan da muka haƙo. Su hau titinan da muka gina. Su ci abincin da muka noma. Su yi gine-gine a kan doron ƙasar da Allah Ya ba mu. Tir da irin waɗannan shashasun ‘yan-Nigeria waɗanda ba su da tunani, ko ma kishin wannan Kasa.

Duk da an san ‘yan ƙalilan ne su a Kudun masu irin wannan gurɓataccen ra’ayi gameda ‘yan-Arewa, amma ɗacin bakinsu ya fara tunzura mutanen Arewa. Haƙiƙa, ba su fahimci alfarmar da ita Arewan take masu ta zamantakewa tareda su ba, ballantana su gode mata. Idan suka kuskura Kasar nan ta rabu, toh kashinsu ya bushe! Lallai ne su shiga taitayinsu tun yanzu, su fi maida hankali wajen neman hanyoyin da Kasar zata ɗore.

Amma kuma, lallai ne mu ce, masu babban laifin barin talauci ya mamaye Arewa ba su fice 'yan

Arewan ba. Mutanen Kudu ba su talauta mu ba; mu muka yi wa kanmu illoli iri iri. Na yi irin wannan magana a baya, inda na sha cewa ba mu yi amfani da baiwoyin da muke da su don inganta arzikin Arewan yadda yakamata ba. Har yanzu haka wannan abu yake. Son-kai da rashin kishin juna, da tsanar da ba gaira ba dalili, suna daga cikin abubuwan da suka azazzala fushi da ƙiyayya a tsakaninmu. Don hakane na yi kira mu zo mu zauna mu duba komai mu san alƙibar da za mu sa kawunanmu. Irin waɗannan halaye namu su suka sa mu cikin talauci da rashin zama lafiya da juna, suka kuma haifar da wannan raini da ake yi mana.

Ba shakka, da 'yan-Arewa zasu bi shawarata ta 5 (a), da babu wani abu da zai tsorata su a Kasar nan. Arewa tana da dukkannin abubuwanda take bukata domin ta bunƙasa arzikinta da na duk al'ummarta da na sauran 'yan Nigeria ma gaba ɗaya. Dá za a duƙufa da gaske da kuma gaskiya a sarrafa arzikin Arewa na Noma da Ma'adinai kaɗai, dá mafi yawan 'yan-Arewa sun yi nesa da talauci; haka sauran 'yan Nigeria a albarkacin Arewan. Muddin dai a Kasa ɗaya muke, mun

yarda su zo su ci daga arzikinmu, kamar yadda suka ci a da cán kafin a sami Man. Amma, ‘kowa ya ci nasa’, wannan aƙidar wasunsu ce. Masu hankali da kishi a Kudun sun san haka. Haƙiƙa, wasu shugabannin a Kudu, suna ba ni kunya, irin zantukan banza da suke ta yi.

A filin Ma'adinai, ba a kama ƙafar Arewa ba a bazuwarsu da yawansu. Ma'adinai irin su Iron Ore, Columbite, Uranium, Tantalite, Tin, Zinc, Kaolin da Coal da sauransu, ga su nan a yalwace a tsabtace a wasu Jihohin Arewa. Sannan ga duwatsun alatu da na ado, irin Sapphire, Emerald, Ruby, Topaz, Zircon, Aquamarine, Garnet, Amethyst da sauransu. A wasu jihohin Arewa na tsakiya da na Gabas, ana samun irin taɓon nan na Bentonite da Barite waɗanda ake amfani da su wajen haƙa da yasar rijiyoyin Mai, wanda shi kansa Man akwai shi fal tun daga Bauchi har zuwa kudancin Tchad a Arewacin Borno. Haka Gold (Dinare) mai kyaun gaske, ga shi nan danƙare a Jihohin Arewa-maso-yamma da na tsakiya. Shirga-shirgan

Duwatsun nan da kuke ta gani tun daga Kaduna zuwa Abuja zuwa Nassarawa da Plateau da Kogi da Kwara, duk dukiya ce mai yawan gaske. Su ne Granite, waɗanda ake yanka ana gyarawa ana amfani da su a ƙawatattun gine-gine. Wasu ƙasashen Turai, irin Italy da Turkey da Greece; da na Asia, irin India da Pakistan da China da Rasha, suna cin moriyar duwatsunsu sosai, kuma suna da masana'antun sarrafa su da sayarda su. A Nigeria, musammam a nan Arewa, muna da launuka har shida ko bakwai masu farin-jini a kasuwar duniya. Su kaɗai babban arziki ne. Amma, muna zaune muna ganin wasu kamfanonin baƙi suna ta yankarsu suna gyarawa suna sayar mana, suna kuma sayarwa ƙasashen waje, ba izni ba haraji! Duk kuma tareda haɗin-bakin wasunmu.

Idan kuma aka dawo wajen Noma, toh, a nan ma babban arzikin Arewan yake. Noman kayan abinci da na sayarwa ba sai an yi maku lissafi ba. Amma dai, an san ko da a noma da cinikin Karo (Gum Arabic) da

Ridi (Sesame), ba shakka Arewa zata iya samun kusan abin da take samu yanzu daga rabon da ake bata daga kasafin kudin shekarar. Yanzu haka, kamfanonin baki ne suke ta cin moriyar Karon da Ridin, muna zaune muna kallonsu. Su saya wajen manomanmu a farashin da suka ga dama; su dauko 'yan kauye su bautarda su, su gyara masu su; sannan su fidda su waje, muna ji muna gani saboda rashin tsari da kishi da azanci. Arewa, ko ma Kasar nan, gaba daya kara zubewa ake yi.

Sannan ga Gyada ga Auduga. Farashin garwar Man-gyada ta ninka ta gubataccen Man-petur tsada a kasuwar duniya. Auduga, kun san ita ce rufin asirin mutum. A Arewa, a da can, dalolin Gyada da masana'antun tace Man-gyadar da na kadar Auduga da na saka, da na Alawa da Biskit, suna cikin ababan alfaharinmu. Ga su nan birjik a ko'ina a Arewa. Yanzu kam kusan dukkannin wadannan masana'antu, na tace Man-gyadar da na kadar Audugar

da na saƙar da sauransu fal a rufe suke, saboda wasu ƙananan dalilai. A da, Kano da Kaduna da Jos da Maiduguri da Gusau, su ne alfaharin Arewa da ita Nigeriar. Ya zama tilas tara jari, mu san yadda zamu gyara unguwannin masana'antunmu, mu kuma farfaɗo da duk masana'antun; a kuma gina sababbi cikin gaggawa. Idan muka yunƙura sosai cikin tunani da ƙwazo, ba shakka, zamu ga alhairi sosai.

A wajen abinci kuma, ga Doya da Dankali da Rogo. Ga Gero da Dawa. Ga Shinkafa da Alkama. Ga Wake ga Masara ga Acca. Ga dabbobi iri iri. Hatta Shanun nan da Fulani suke kaiwa Kudu, dá naman kaɗai zasu kai, dá kuɗin da zasu samu a ƙasusuwan da fatun da ƙahonnin, dá sun yi daidai, ko ma fin kuɗin naman shi kansa. Kasusuwan kaɗai, arziki ne in an sarrafa su; ballantana kuma Kiragan. In an tuna, a da, ciniki da masana'antun jimar Fatu da Kiraga, ba ƙananan masana'antu ba ne da kasuwanci a gida da waje. Amma sai

Fulani su kora dabbobi masu yawan gaske, ba sa la'akari da wahalar tafiya da kiwo da ‘yan fashi da mutuwar dabbobin a hanya, ballantana muguwar hasarar da suke yi ta karyar da farashin dabbobin a can. A Arewa, muna da Mayanku na zamani da gyara nama don sayarwa a gida da waje, kuma lallai ne a ilmantarda waɗanda basu sani ba.

Noman Shinkafa da Alkama kuwa, dá zamu tsaya mu yi sosai, dá abinda za a noma (a tsakanin Arewa ta tsakiya da Arewa maso Yamma kaɗai) zai iya ciyarda Africa gaba ɗayanta. Su Tattasai da Barkono da sauran kayan miya, ba a cewa komai, ballantana a ce zamu sarrafasu a masana'antu a sayar a cikin gida da waje. Kai, hatta dabinon da kuke gani, dá Arewa zata maida hankali a kansa shi kaɗai, dá ba ƙaramin arziki jama’a zasu yi ba. ‘Ya’yan itatuwa birjik suna nan suna jiran ‘yan-Arewa su fahimci muhimmancinsu da yalwarsu a jihojinsu.

> Faɗin ƙasa kaɗai, ba ƙaramin abu ba ne. Ba wanda ya san wannan fiye da ‘yan-Kudun.

Ba abinda ba mu da shi na bukata da gina arziki a nan Arewa, illa juriya da fafutuka. Lalaci da son banza sun yi yawa. Waɗannan ɗabi'u su zamu tsaya mu yaƙa, mu yi watsi da su; mu haɗa kawunanmu mu nemo arzikinmu, mu kuma dawo da mutumcinmu a junanmu da Kasar. Ba abinda za a yi ana kwance. A wannan zamani, sai ka shara da gudu tukuna, sannan zaka iya kasancewa inda kake. Ko kuma a tafi a barka.

Tabbas, ba na ɗaya daga cikin masu yayata son a raba wannan Kasa tamu, domin na san dá kawunanmu a haɗe suke da sanin yakamata a tsakaninmu, dá ba haka ba. Shekarun baya, an ji ‘wai’ wasu suna cewar an kusa korar Arewa daga Nigeria. A tabbata mahaukatan suna wannan magana ne don zaton Arewa ba ta da komai, ko ba ta shirya ba, ko duk biyun. Amma an san masu yin wannan barazana ga Arewa, ba su san yadda irin wannan rashin hankali da

rashin kishin Kasa nasu zasu zame masu babbar illa ba.

> Abinda ba sa tunani a kai shi ne, idan muka zama ƙasashe dabam, ‘yan-Arewa da yawa suna cewa tilas kowa ya koma ƙasarsa. Suna cewa take ma Arewa zata fice daga yarjejeniyar Ecowas don kada ma a laɓe da ita. Haƙiƙa, bai kamata wani ya sake zubarda jininsa, ballantana ransa, don kada Nigeria ta rabu ba. Gara a rabu lami lafiya, mu zama maƙwabta masu zaman lafiya da cinikayya da juna, da a ce mun sake yaƙin basasa. In har wancan bai koya mana hankali ba, na gaba ba mu san iyakacinsa da na lahaninsa ba. Mu yi fatan kawai, Allah Ya taimakemu Ya bar mu tare, Ya sa mu gane abubuwan da nake faɗa cikin tunani da fasaha da kishin juna.

Amma, idan rabuwa ta zamto tilas saboda ba a sonmu, wadda ba na fata, amma wadda wasu marasa tunani suke azazzalawa, toh, lallai ne su san sharri ce a garesu. A Arewa, lallai ne a ci ƙarfin duk ɓurɓushin ƙiyayya tsakanin

al’ummanta, yadda zata koma Arewa irin ta da cikin zaman lumana da arziki; a cikin Kasa mai sarari babu sauran cunkoso. Mutanenta, da samarinta su sami aikin yi, su zama su ne maginanta, su ne masu aikin lantarki, famfo, gyaran mota da injina. Su ci ribar kasuwanninta ta kowanne fanni. Su zama su ne lauyoyinta, su ne akantocinta. Haƙiƙa, a Kasa ɗaya, ‘yan-Kudu ma suna da 'yancin su yi duk waɗannan domin ko’ina ƙasarsu ce, kuma ni na sha jan hankalin cewar lallai ne duk ɗan-Nigeria ya wataya a Kasarsa ba tareda da wata ƙyama ko tauye dáma ba. Kuma har yanzu haka abin yake, saboda ina matuƙar son wannan Kasa, kuma na san dá zamu cuɗi juna a ko’ina da soyayya, mu zauna lafiya, dá ƙasashen da zasu iya kamo Nigeria a duniya wajen arziki, kaɗan ne. Yanzu kam, muna cikin koma-bayan ƙasashe da yawa.

Amma, a nazarin wasu a Kudu, suna ganin Arewa ba ta shirya ba; kuma suna zaton Arewa ce mai hasara in Kasar ta rabu. Wasu da suka karɓi ragamar mulki sun yi duk ƙoƙarin da zasu yi su hana Arewa shiryawa ta hanyar tauye arzikinta da ƙin gina abubuwan da suka kamata

a gina saboda ci-gabanta. Sun ce ma Arewar Hamada ce! Amma, idan Arewa ta tashi haiƙan, cikin ɗan lokaci ƙanƙani zata iya shiryawa, ta sami ƙasashen da zasu taimaka mata, su tallafeta shekara biyar zuwa goma har sai ta tsaya da ƙafafunta, domin tana da duk abubuwan da suke bukata, waɗanda zasu kwaɗaita masu alhairan taimakawar da zasu yi wa Arewar. Akwai waɗanda ma zasu taimaka wa Arewar kyauta; akwai kuma waɗanda zasu bukaci wani abu kaɗan a gurinta. Ko nawa, ko me kuma take bukata zasu iya bata har zuwa wasu shekaru da suka dace. A wannan, ba shakka ko kaɗan. Sai dai in mutanen Arewar ba su tashi neman da gaske ba.

Masu hikimar gina zaman lafiya a tsakanin ƙasashe sukan ce: Kasashe sukan kai hari ne kaɗai ga ƙasashen da suka raina, suke kuma ganin damarsu domin basu kai ƙarfinsu ba. Saboda haka, idan kowa ya gina ƙarfinsa yadda idan aka ce masa 'kule', zai iya cewa, 'cas', toh sai a zauna lafiya. Wannan shi ne da turanci ake kira, "deterrence". Ashe in hakane kuwa, daidaituwar arziki da ilimi ma a tasakanin

ɓangarorin Arewa da na Kudu, zasu iya tabbatar da zaman lafiya da juna a wannan Kasa tamu ta Nigeria.

Ba shakka, ganin akwai talauci da jahilci da ɗimbun jama'a marasa aikin yi a nan Arewa, shi ya sa wasu ke ganin damarmu. Amma, dalilin jahilcin da talaucin namu, shi ne zama kara zube da muke yi a Arewan ba ƙididdiga ba tunani.

Rashin kulawa da damuwa ya sa kowanne shawaraki da kowacce shara, nan Arewa take yowa daga kowanne ɓangare na wannan Kasa tamu. Sai an tara da tamu sharar da shawarakan sannan za a fara ganin yadda rashin shugabancin da rashin alƙiblar suke illatarmu, musammam ma kuma wajen rashin tsaro da rashin ƙiddigar muhimman abubuwan auna rayuwa ta ƙwarai. Yawancin birane da ƙauyuka a Arewa a hargitse suke. Wasu ma sam-sam ba a san ko su waye ba, ballantana daga ina suke. Yawanci ma dai, ko maƙwabtanmu ba mu sani ba, ballantana mu san dalilin zuwansu da na zamansu da abubuwan da suke ƙulle da su. Amma, idan muka zauna muka faɗawa kanmu gaskiya, muka yi shiri da tsari

ingantattu kamar yadda na ba da shawara a can baya, toh ba shakka, zamu iya nema, mu kuma sami masalahar dukkanin wahalunmu da illolin da suke addabarmu.

Nigeria, ƙasa ce wadda aka haɗata ba tare da an yi wasu yarjejeniya da aka tsara kowa ya yarda dasu ba. Turawa ne kawai suka yago nan da can suka haɗa, suka ce mana, 'ku ne Nigeria'; mu kuma muka ce, 'toh, mun yarda'; alhali ba mu yarda da junanmu ba. Sam sam, ba mu auna bambance bambancenmu na al'adu da salon ilimi da na mulki da na sana'o'i da na addinai da tarihi ba; ballantana kuma na irin tarbiyoyin da kowa ya samu. Nigeria, cakuɗin ƙasashe ce da al'adu masu ƙarfin gaske, waɗanda suke bukatar su fahimci juna. Amma sai muka taho cikin munafurci da ƙiyayya ta ɓoye da ta sarari, muna fatan mu kasance Kasa ɗaya. Toh, kasancewa al'umma ɗaya fa? Ko taken N.P.N. (Kasa ɗaya; Al'umma ɗaya) fata ne kawai shi ma.

Tun a shekarar 1986, a wani littafina (In Search of Unity) wanda ban buga ba, na ce, "Nigeria, Kasa ce hautsune da ƙasashe da al'ummai masu

yawa. Har yanzu ba mu zama Kasa ɗaya ba a zahiri, sai dai a tunani. Ya zama tilas duk ɓangarorinta su zauna su tattauna, su yarda su zama tare cikin Kasa ta gaskiya, wadda suka amince da tsarinta a shimfidar ƙa'idoji da yarjejeniyoyin da suka yarda da su.” Ina ganin wannan ya taunawa ta zama tilas, musammam ma a yanzu.

Wannan littafi yana nan. Duk mai son gani ya zo zan nuna masa shi. Kuma zan farfaɗo da shi nan gaba.

Lallai ne 'yan-Arewa su daina jin tsoron wannan tattaunawa da wasu jinsinan Kasar nan suke ta koɗawa sai an yi. Kiran da wasu a Kudu suke ta yi cewar lallai ne a zauna a daddale a taron da ake kira da turanci, **"Sovereign Conference",** ba illar da zai yiwa Arewa. Kuma, ni yanzu na yarda sun yi tunani mai zurfi a kan wannan al’amari. Ni na goyi bayansu a yi wannan taro, domin kowa ya san matsayinsa da dalilin da ya sa yake zaune cikin wannan Kasa, tareda haƙƙunansa da kuma nauyin da yake kansa. Ta irin wannan yarjejeniya da fahimta ne kaɗai

dukkaninmu zamu iya zama tare cikin lumana. Duniya ba tsaye cik take ba. Kuma, idan iskar canji ta buso, ko ka tafi da ita, ko kuma ta tafi da kai.

Idan ma kowa gashin-kansa kawai zai ci; har da yadda izinin zama a ɓangaren da ba naka ba zai kasance; ko yadda za a yi sufuri da cinikayya da juna; ko ma yadda za a sake tsarin mulki irin na “zaman tare ba tare ba”, yadda wasu ke cewa, “Confederation” a turance; ko me ma ake son a yi har da rabuwar, toh, a yarda da hakan da ƙa’idojin da sharuɗɗan da zasu tabbatar da hakan, ba cuta ba cutarwa. Hakan ne zai fi mana alhairi da wannan zama na munafurci da ƙiyayya da danniya da raini da sauran ababan takaici barkatai ga juna.

An san mu dai Arewa a halin yanzu, ba zamu ce ba ma son Nigeria ba, saboda mu ne ita, ita ce mu. Amma duk lokacin da aka kore mu, ko muka gaji don kanmu, toh ba shakka, zamu ta fi salun alin. Amma kuma a tabbata mutanen Arewa ba zasu yi wata nawa wajen cewa tilas ne su ma a bar masu Kasarsu nan take ba. Watau

dai, kowa ya koma Kasarsa, ya yi abinda yake so ba tsangwama. Ba wanda zai ci a nan ya kuma ci a can. Wannan kam ba zata yiwu ba. Duk mai tunanin za a raba Nigeria, ya ci gaba da miƙe ƙafa a ƙasar da ba tasa ba, gara ya manta ya fara shiri. Masu cewa Arewa kaska ce ga Nigeria, lallai su san sun yi kuskure babba.

Ko kuma jita-jitar da muke ji cewa wasu Kasashen waje sun yi hasashen rabuwar Nigeria a 2015 tana da tushe ne? Ko kuma duk wannan barazana da ake yiwa Arewa tana cikin wannan shiri ne? Ko kuma duk wannan taɓargaza da ake ta yi duk shiri ne na wasu don a nuna zama taren ba zai yiwu ba? Ko kuma wani shiri ne na tarwatsa Arewan ita kanta? Lallai akwai tuwon tunani a cikin waɗannan abubuwa da suke ta faruwa.

Ba shakka, Nigeria tana da nata maƙiyan!

A rayuwata ta siyasa da mu'amulla, na san 'yan Kudu da yawan gaske. Ina da abokai, mutanen kirki, masu mutumci, masu son Kasar nan, waɗanda suke ƙauna suke kuma bautawa Kasar nan kamar kowa. Wasu da yawa cikinsu abokan

kasuwancina ne; wasu kuma na siyasa; wasu ma sun ɗauke ni tamkar ɗan'uwa saboda daɗewar sanayya da juna.

Na tabbata zantattukan waɗancan shawarakai, 'yan tasha a cikinsu, ba abu ne da suke so ba. Amma fa, ban ji su suna tsawatarwa ba. Haka kuma, akwai wasu shawarakan a nan Arewar su ma suna irin wannan zance na matuƙar rashin hankali; wai basa son musulman Arewa. Toh, su ɗauki gidajensu ko ƙauyukansu su maida su can Kudu, in zasu iya. In ba zasu iya ba, toh su tashi su koma can su kansu. Allah ya raka taki gona.

Allah wadan naka ya lalace!

LA'AKARI

Ba yadda za a yi rubutu a kan illolin da suke ta ƙalubalantar Arewa da Kasar nan, ba a sa Rashin Shugabanci na gari da Rashin Adalci da Sata da Rashawa (corruption) da tsadar Gwamnati (yawan Ministoci da Majalisun Tarayya da zaɓaɓɓu da ma'aikatan Gwamnatoci da nadaɗɗun 'yan-siyasa) da tsadar Kwangiloli ba. Haƙiƙa, waɗannan suna cikin ummul-aba'isin mishikilolin Nigeria. Irinsu ne suka haifarda talauci, wanda yake husata jama'a, har ake ganin ba a da makoma, ko kuma wasu ne suka danne wasu. Dá za a tashi a yaƙi waɗannan illoli, dá abubuwa da yawa sun canja. Suna cikin abubuwan da suka sa ake zancen 'Sovereign Conference' da 'Resourse Control'. Yanzu ya zama tilas a yi la'akari da nazari a kan waɗannan.

KARASHEN MAGANA

Wancan taro na ‘yan-Arewa yanzu ya zama tilas a yi shi kuma da gaggawa. Idan muka fahimci kanmu, muka shirya da junanmu, muka san ƙarfinmu da arzikinmu, toh kuwa lallai zamu san cewa ba wani abu da zamu ji tsoro a wannan Kasa tamu. Haka su kansu ‘yan Kudun. Idan a Nigeria gaba ɗaya, muka kasance masu tunƙaho da ilimi da arziki (ko da kowa nasn kawai yake ci), muka kuma amince da duk yarjejeniyarmu, muka yi la'akari da ƙa'idoji da sharuɗɗan zamanmu tare, toh sannan ne kaɗai wannan Kasa ta Nigeria zata zama Kasa ɗaya mai ƙarfi, tabbatacciya, mai al’umma haɗaɗɗiya. Sannan ne kuma zata ɗauki matsayinta na girma a cikin ƙasashen duniya, ba tareda tana shakkun kanta ba. Sannan ne arzikinmu zai ƙarfafa, iliminmu da ci-gabanmu su zama ‘gidan-kowa da akwai’; mu kuma iya tsere da ƙasashe sa’anninmu irin su Singapore da Thailand da Malasia da Indonesia da Taiwan; waɗanda ake kira “Damisoshin Gabas”.

Mu kam, mu ne “Muzuran Kudu”. Yau ga shi hatta ƙasashen Gabas-ta-tsakiya ma duk sun bar mu a baya saboda sakacinmu.

A wasu shekaru can baya, da yawa a cikin ƙasashen Larabawa na Gabas ta Tsakiya da Afrika ta Arewa, duk a bayanmu suke. Amma, yau fa?

Haka kuma, a tsakanin shekarun 1975 da 1980, Nigeria ce ta taimakawa Malaysia, ta ba ta ‘iri’ ta koya masu yadda zasu noma ‘irin’ da ake tatsar Manja (Palm Oil) daga ‘ya’yansa. Yanzu Malaysia ita ce gaba a noma da sayar da Manja a duniya. Muna zaune muna gani. Haka abubuwa da yawa suke. Ku dubi harkar Gurbataccen Man. Nan gaba kaɗan, sai ƙasashen Ghana da Niger sun shige mu, muna shashanci da ta’asa da ɓarna.

Saboda haka, idan muka ci gaba da zama a watse; a Arewan da Kudun, muka bar talauci da jahilci a wasu jihohinmu da gangan, ko don mugunta; muka ci gaba da tsangwama ga juna toh, wataran sai marasa kuɗin da marasa ilimin da waɗanda ake tsangwamar, sun yi katoɓarar da

zamu daɗe ba mu warke ba. Irin tarzomomin da ta'addan da ake ta yi a jihojin Kaduna da Plateau da Borno da Yobe da Bauchi da can Kudu-maso-Kudu, da aka sa wasu suke maƙalawa Musulmai su kaɗai, idan ba mu yi hankali ba, su ne zasu yi ambaliya da wannan Kasa tamu. Kuma duk a yi da-na-sani.

TUNATARWA DA FATAN ALHAIRI

A can baya a shafuna na 40 da na 53, na yi zancen abinda wasu a Kudu suke ta magana a kai, watau, **"Resource Control"** (kowa ya ci nasa), da kuma, **"Sovereign Conference"** (taron sake lalen zama-tare) a wannan Kasa.

Lallai ne mutanen Arewa su tashi su shirya yadda zasu tunkari waɗannan abubuwa, domin suna tafe, kuma sai an sa su a baya za a zauna lafiya. Lallai ne mutanen Arewa a kowacce Jiha, su shiga tattaunawa cikin tsari, kuma gaba ɗaya a ɗau matsayi a kan kowannensu. Kar a sake a zaune shirim ba shiri. Lallai ne Gwamnonin

Arewa da sauran shugabanni su fara tattaunawa a junansu, sannan su kafa kwamitoci masu ƙarfi na masana, jarumai a Jihohinsu, domin su duba dukkannin waɗannan abubuwa tun yanzu, su ba da shawara.

Ga ‘yan-Arewa, ya fi zama wajibi mu fara wannan tattaunawa da tsari a kan junanmu kamar yadda na ba da shawara can baya (sh. 36-38), tun kafin mu fuskanci Kasar a waɗancan tarukan, da murya ɗaya ta Arewa, wadda kowa zai jita ya san mun canja; mun shirya.

A ra’ayina, lallai ne a sami karɓaɓɓen matsayi wanda zai tabbatarwa ‘yan-Arewa da ‘yan-Kudu daidaituwa a kowanne fanni na zamantakewa da cin arziki da mulki a Kasar nan. Kada a bar wata kafa wadda zata sa wani ya ji cewar wani yana cutarsa ta kowanne irin fanni.

Lallai ne daga ƙarshe, duk ɗan Nigeria ya ji cewar ana yi masa adalci a duk inda yake, ba cuta ba cutarwa. Akwai abubuwa masu yawan gaske da sai an duba an gyara su. Wannan gyran, shi ne ma zai taimaki Arewan.

Idan an gama a cimma yarjejeniya, lallai ne kowa ya gamsu da abubuwan da aka yarda da su. Sannan sai a kaiwa Majalisun Jiha da na Tarrayya su duba, su kuma sa gyararrakin a cikin Konsitushin ta Kasa. Ta hakane kaɗai zamu zauna lafiya, mu kuma zama masu kishin kanmu, mu guji yi wa juna habaici da tsangwama, mu kuma ci arzikinmu a sikelin adalci.

Ta haka ne kaɗai dukkaninmu a Nigeria, zamu zama masu kishin wannan Kasa tamu, mu kuma kasance, "**Kasa ɗaya**" wadda zata iya cimma burinta na, "**Al'umma ɗaya**", a haƙiƙa ba a fata kaɗai ba. Lallai ne mu farga tun kafin lokaci ya ƙure mana, ganin yadda abubuwa suke a yau.

